

HA

# “Ina cikin tsarin Dublin – menene wannan yake nufi?”

B

Bayanan ga masu neman daman na kariyar kasa da kasa wanda aka sama tsarin Dublin, daidai da yankin kundin Doka (EU) na 4 mai lamba 604/2013

**An baka wannan takarda takaitaccen bayani ne asabo da ka nemi kariyar kasa da kasa (neman makafa) a wannan kasa ko a wata kasar Dublin ta daban kuma wannan hukumar tana da dalilin yarda cewa wata kasa ce kila ke da hakin bincika bukatarka.**

**Za mu bincika wace kasace ke da hakin ta wata hanya da dokar Kungiyar hadin kain Tura wadda aka fi sani da Dokar 'Dublin' Ana kiran wannan shiri da suna 'Tsarin Dublin'. Wanna takardar takaitaccen bayani na zaman amsa ga mafi yawancin tambayoyi da kake dasu game da wannan tsari.**

**Idan akwai wani abu a rubuce anan da baka fahimtaba, ka tambayi hukumar.**

**Wannan takardar takaitaccen bayanai tana ba da bayani ne kawai. Burinta shine samarar da bayanai ga masu neman kariyar kasa da kasa a game da Tsarin Dublin. Ba ta kirkira/kumshi dama ba da kanta ko doka Damar da hakki na Kasashe da mutane a karkashin tsarin Dublin sun kasance a Dokoki (EU) 604/2013.**

**©European Union 2014**
**An amince sake bugawa. Dole ne a nema samin dama daga masu ikon bayar da dama domin anfani ko sake buga hoton wani mutum**




*Wadannan kasashen Dublin sun hada kasashe 28 na Hadin kan Turai (Austria (AT), Belgium (BE), Bulgaria (BG), Croatia (HR), Cyprus (CY), Czech Republic (CZ), Denmark (DK), Estonia (ET), Finland (FI), France (FR), Germany (DE), Greece (EL), Hungary (HU), Ireland (IE), Italy (IT), Latvia (LV), Lithuania (LT), Luxembourg (LU), Malta (MT), Netherlands (NL), Poland (PL), Portugal (PT), Romania (RO), Slovakia (SK), Slovenia (SI), Spain (ES), Sweden (SE), United Kingdom (UK)) har da kasashe hudu "masu alaka" da Dokar Dublin (Norway (NO), Iceland (IS), Switzerland (CH) da Liechtenstein (LI)).*

## “Mai yasa nake cikin tsarin Dublin”

Dokar Dublin tana aukuwa a gaba daya wani yanki wand ya hada da kasashen 32. **‘Kasashen Dublin’ sun hada da:** Austria, Belgium, Bulgaria, Croatia, Cyprus, Czech Republic, Denmark, Estonia, Finland, France, Germany, Greece, Hungary, Ireland, Italy, Latvia, Lithuania, Luxembourg, Malta, Netherlands, Poland, Portugal, Romania, Slovakia, Slovenia, Spain, Sweden, United Kingdom) har zuwa tare da kasashe 4 “da ke da alaka” da yankin Dublin (Norway, Iceland, Switzerland da Liechtenstein).

Tsarin Dublin yana kirkirar wace kasa daya ce wadda ta ke da hakkin bincika takardar neman dammar samun makafarka. Wannan na nufin za a iya dauke ka daga wannan kasar zuwa zuwa wata kasa ta daban da ked a hakkin bincika takardar neman damarka.

Tsarin Dublin yana da dalilai guda biyu:

- domin tabbatar da cewa takardar neman dammar samun makafarka za ta isa ga hukumar kasar da ked a hakkin bincikata.
- Domin tabbatar da cewa baka nema damar samun makafa fiye da sau daya ba a kasashe daban daban tare da burin tsawaita lokacin zamanka a kasashen Dublin.

Har sai an shawarta wace kasa c eke da hakkin yanke shawara akan takardar neman damarka, wannan hukumar ba za ta kula da bayanan cikin takardar neman damarka ba.

**TUNA**: Bai kamata ka tafi zuwa wata kasar Dublin kuma ba. Idan ka tafi zuwa wata kasar Dublin, za a dawo da kai nan ko wata kasa da ka taba neman mafuka. Barin takardar neman damarka anan ba zai canja kasar da ke da hakkin ba. Idan ka boye ko ka gudu, za ka fuskanci barazanar kasanewa a gidan kaso

Idan ka taba kasancewa a cikin wata kasa daga cikin kasashen Dublin kuma tun sannan ka bar yankin kasashen Dublin kafin ka zo wurinmu, dole ka gaya mana. Wanna yana da mahimmanci domin zai ya samar da wace kasa c eke da hakkin bincikar takardar neman damarka. Za a iya




©European Union

bukatar ka samar da shaidar lokacin da ka kasance ba a ckin kasashen Dublin ba, misali tabari akan passport dinka, takardar yakinin dawowa ko ta fitarwa ko takardar hukuma da ke nuna cewa ka zauna ko ka yi aiki a wajen kasashen Dublin din.

## “Wane bayanai ne zan tabbatar cewa hukumar ta sani?” “Yaya zan yi bayanin wannan labari ga hukumar?”

Akwai yiwuwar za a yi maka tambayi (tambayoyin kanka) domin gano wace kasa ce ke da hakkin bincika bukatarka ta neman makafa. A wadannan tabayoyin, za mu yi bayani game da ‘Tsarin Dubin’. Ya kamata ka sanar damu duk wani bayani da kake da shi game da wani daga chikin iyalinka ko dan’uwa a cikin daya daga cikin kasashen Dublin, tare da duk wani bayani da kake tunanin yana da anfani domin gano kasar da ke da hakkin (kalla kasa domin cikakkar alama yayanin da ke da mahimmanci). Kana kuma bukatar ka samar da duk wata takarda da ke tare da kai da ke dauke da muhimman bayanai.

**Don Allah ka fada mana duk muhimman bayanai domin taimaka mana gano kasar da ked a hakkin bincikar takardar samun damarka.**

Tambayoyin za su kasance a harshen da ka fahimta or ko kuma ya kamata ka fahimta da zance das hi.

Za ka iya sanya tafunta ya taimaka maka idan ba ka fahinci harshen ba. Mai fassaran zai fassara abin da kai da mai tambaya kuke fadi ne kawai. Tafuntan ba zai kara nashi ko nata ra’ayuka ba. Idan kana da matsala wajen fahimtar maifassarar, lallai ka gaya mana ko ka gaya wa mai shara’arka.

Za sirranta tambayoyin. Wannan na nufin babu daya daga cikin bayanan da ka bayar, tare da kasancewa ka nemi dammar samin makafa, da za a aika zuwa ga wani mutum ko hukuma a kasarka ta asali wanda zai iya cutar da kai ko ta wace hanya, ko kuma wani daga cikin iyalanka da ke zaune a kasarka ta asali.

Za a iya hana ka dammar tambayoyi ne kawai idan ka riga ka samar da wadanna bayanai ta wata hanya, bayan ka sama bayanin tsarin Dublin tare da matsalolin shi a halin da kake ciki. Idan ba a yi maka tambayoyiba, za ka iya bukatar samar da Karin rubutaccen bayani da ked a anfani domin gano kasar da ked a hakki.

## “Ta yaya hukumar za ta samar da kasar da hakkin binchika takardar neman damata? “

Akwai dalilai da dama da suka wata kasa za ta kasance da hakkin bincika takardar neman damarka. Ana aiwatara da wadannan dalilai a jere game da mahimmanci da shari’a ta basu. Idan dalili daya bai da muhimmanci, za a duba na gaba, haka haka.

Dalilin na da alaka da abubuwan da ke tafe, game da muhimmancinsu:

- Kana da iyali (miji ko mata, yara kasa da shekaru 18) wanda aka samarwa kariyar kasa da kasa ko kuma yana neman makafa wata kasa ta Dublin;

  **Yana muhimmanci ya kasance ka sanar damu idan kana yan’uwa a wata kasa ta Dublin, kafin a yanke shawarar farko game da bukatar neman makafarka**. Idan kana so a kawo ku tare a kasa daya, sai kai da dan uwanka kun bayyana a rubuce.
- Wata kasa ta Dublin ta taba baka visa or damar zama;
- An dauka alamun yatsunka a wata kasar Dublin (an kuma adana su a ma’adanar bayanan Europe mai suna Eurodac [1]);
- Akwai shedar cewa ka taba zuwa, ko kuma ka wuce ta cikin, wata kasar Dublin, ko da ba a dauka hoton alamun yatsunka ba.




1) **Akwai Karin bayani game da Eurodac a shafi na 8 na takarda mai takaitaccen bayani “Na nema makafa a EU – wace kasa ce za ta rike bukatata.**

## “To yaya idan na dawwama da kulawar wanine ko kuma wani ya dawwama dani?“

Zak u iya sake hadewa a kasa daya kamar **mahaifiya, mahaifi, da/ya, kani ko kanwa** ida sauran sharuddan sun kamala:

- Suna zaune ne bisa doka a cikin daya daga cikin kasashun Dubkin;
- Daya daga cikinku na da ciki, ko na da sabon jariri, ko na tsananin rashin lafiya, ko na da nakasa ko tsufa;
- daya daga cikinku ya dawwama da taimakon daya, wanda yake kulawa dashi ko ita.

Lallai ne kasar da dan/yarka, kani/kanwa ko mahaifi/mahaifiya ke zaune ta kasance tana daukar nauyin hakkin bincika takardar neman damarka, mayukar zumunci yan’uwanka ya kasance tun a kasarku ta asali. Za a bukace ku da ku bayyana a rubuce cewa ku biyu kuna so ku sake hadewa tare.

Kana iya bukatar wannan damar idan dama kana zaune ne a kasar dad an/yarka, kani/kanwa ko mahaifi/mahaiya ke zaune, ko kuma idan kana zaune ne a wata kasa ta daban da wacce yan’uwanka ke zaune. A cikin wannan uziri na biyu, yana nifin cewa za ka yi balaguro zuwa wancan garin, sai dai idan kana da wata matsalar lafiya wadda ta hana ka yin balagurohar na tsawon lokaci.

Kari da wanna maiyiwuwa, kana iya bukata hadewa da danginka domin taimako, dangantaka or dalillai na al’ada. Idan an aminta da wann, to za ka tafi zuwa kasar da danginka suke. A irin wannan yanayi za a bukaci ka bayar da amincewarka a rubuce. Yana da muhimmanci ka sanar da mu game da duk wani dalilin taimako domin samin bincika bukatarka a wannan kasa ko wata kasa ta daban.

**Idan aka tayar da maganar dangantaka, dangana, ko taimako za a iya bukatar ka da bayar da bayani ko shaida domin goyon baya hakikaninka.**

## Menene idan bani da lafiya ko ina da wata bukata ta musamman?

Domin a samar maka da kulawa da lafiya mai inganci ko jinya, hukumominnan na bukatar sanin duk wata bukata ta musamman da kake da ita, tare da tare da bayanin lafiyarka, da kuma idan muasamman idan ka:

- kasance nakasasshe,
- kasance mai ciki,
- kasance mai tsananin rashin lafiya,
- fuskanci azabtarwa, fyade ko wasu nau'in tashin hankali da suka shafi tunani, jiki ko jima'i

Idan ka gaya mana cikakkun bayanai lafiyarka kuma aka shawarta cewa za a aika da kai zuwa wata kasa ta daban, za mu bukaci izininka domin raba bayanan lafiyarka tare da kasar za a aika da kai. Idan baka aminta da wannan ba, wannan zai hana aikawa da bayanan lafiya, ammma ba zai hana aikawa da kai zuwa kasa da ke da hakkin ba. Ka sani cewa idan ba ka amince da bari mu aika da bayanin lafiyarka zuwa wata kasa ba, wata kasar ba za ta iya kulawa da bukatun ka na musamman ba.

Ka sani cewa shahararrun ma'aikata za su rike bayanan lafiyarka tare tsananin sirri

## “Wane tsohon lokaci zai dauka kafin a shawarta wace kasa ce za ta bincika takardar neman damata? Wane tsawon lokaci zai dauka kafin a bincika takardar neman damata

Idan hukumomin wannan kasar suka shawarta cewa mu ne m ke da hakkin kbincika takardar neman damar makafarka, wannan yana nufin cewa za ka saura a wannan kasa kuma a bincika takaradar neman damarka a nan.

## “Menene zai faru idan wata kasa, daban da inda nake, ta kasance ita ce da hakkin bincika takardar neman damata?”

Idan muka duba cewa wata kasa ce ke da hakkin bincika takardar neman damarka, za mu bukaci waccar kisar da ta dauki hakkin a tsakanin **watanni 3** na kwanakin watan da aka ajiye takardar neman damar ka a wannan kasa.

Ko yaya, idan an samar da hakkin wata kasa a sanadiyar bayanan zanen yatsunka, za a aika bukatar ta waccar kasa a tsakanin **watanni 2** daga lokacin da aka samo sakamakon bayanai daga Eurodac.

- *Idan wannan shine karo na farko da ka nemi damar samin makafa a kasar Dublin amma kuma kana da dalilin da yasa kake so a yarda wata kasar Dublin ta bincika takardar neman damar makafarka, za mu bukaci cewa wata kasa ta* ***“dauki hakkin”*** *bukatarka.*

Dole ne kasar da muka aika wa da bukatar ta ansa tsaknin **watanni 2** da samin bukatar. Idan waccar kasar ba ta ba da martani ba a cikin kayyadadden lokacin, wanna yana nufin cewa ta aminta da daukar hakkin neman damarka.

- *Idan dama ka taba neman makafa a wata kasar Dublin ta daban da kasar da kake ciki yanzu, za mu bukaci waccar kasar ta* ***mayar da kai”***

Dole ne kasar da muka aika wa da bukatar ta ansa tsaknin **wata 1** na karbar bukatar ko tsakanin **sati 2** idan bukatar ta ta’allaka da bayanan Eurodac. Idan waccar kasar ba ta ba da martani ba a cikin kayyadadden lokacin, wanna yana nufin cewa ta aminta da daukar hakkin neman damarka kuma ta yarda ta mayar da kai.

Idan, ko yaya, ba ka nema damar samin makafa ba a wannan kasar kuma kuma an soke neman damarka na da a wata kasa ne a matakin karshe, za mu iya zabar aikawa da wata bukata zuwa ga kasar da ke da hakkin

ta mayar da kai, ko ta ci gaba da mayar da kai zuwa kasar ka ta asali ko mazaunin dindindin ko kasa ta uku mai kariya.

Idan wata kasa ta aminta cewa tana da hakkin bincika takardar neman damarka, za a sanar da kai shawarar da mu ka yanke:

- kada a bincika bukatarka ta neman makafa a wannan kasa da,
- a mayar da kai zuwa kasar da ke da hakkin.

Mayarda kai zai auku cikin watanni 6 na kwanan watan da wata kasar ta aminta hakkin, ko, idan kana so ka yi korafi game da shawarar, tsakanin watanni 6 daga yanzu wata kotu ko wakilan shara'a suna yanke shawara cewa za a iya mayar da kai zuwa waccar kasar. Za a iya tsawaita wannan takaitaccen lokaci idan ka gudu daga wannan hukumar ko idan kana kaso.

Idan kana a kulle / wata cibiyar kulle a wannan kasa a zaman yankin tsarin Dubin, za a sanya akaitaccen gajeren lokaci (Duba sashe na musamman akan kulle domin karin bayani).

Kasar da ke da hakkin za ta kula da kai kamar mai neman makafa kuma za ka ci anfanin duk wata dama da ta dangaceka Idan baka taba neman damar samin makafa ba a waccar kasar, za a baka dama ka nema dama bayan isarka.

## “Mene idan ban yarda da shawarar aika ni zuwa wata kasa ba?”

Kana da yiwuwar cewa baka yarda da wata shawarar aikawa da kai zuwa wata kasar Dublin ba. Ana kiran wannan ‘daukaka kara’ ko ‘sake dubawa’ Za kuma ka iya bukatar janye maidawar na tsawon lokacin daukaka kar ko sake dubawar.

Za ka iya samin bayanai game da wace hukuma ce ya kamata a tuntuba domin kin amincewa da wani hukumci a wannan kassar a karshen takardar takaitaccen bayani.

Idan ka karba hukumcin mayrwan daga hukumomin, kana da kwanaki 21 domin daukaka kara a Kotun Gudanarwar. Yana da matukar muhimmanci cewa ka ki aminta da (daukaka kara ko sake dubawa) a tsakanin kayyadadden lokacin.

Kana da kwanaki 7 domin bukatar cewa a dakatar da shirin mayar da kai yayin da ake bincika daukaka kararka. Wata kotu ko majalisar masu shari’a za ta yanke hukumci akan wannan bukata a cikin takaitaccen lokaci. Idan ta hana ka janyewar, za a baka dalilin haka.

Kana da damar taimaon maisharia a yayin wannan kuma, idan kana bukata, taimakon gwanin harshuna. Taimakon mai sharia na nufin za ka iya daukar lauya wanda zai shirya takardun ka kuma ya wakilce ka a kotu.

Zaka iya bukatar samin wannan taimako a kyauta idan ba za ka iya biyan kudin ba. Za a iya samin bayani game da kungiyoyin da ke bayar dataimakon sharia a karshen takarda takaitaccen bayani.




©iStockphoto / Joe Gough

## “Shin ba za a kulleni ba. “

*Akwai wasu dalilai da yasa ba za a kulle ka ba, amma, domin tsarin Dublin, za a iya kulle ka idan hukumomin mu suka fahimci cewa a kwai hadari za ka iya guduwa saboda ba ka so a kai ka wata kasa ta Dublin.*

## “Menene wannan yake nufi? “

Idan hukumomin suka lura cewa akwai babban hadari cewa za ka iya guduwa daga wurin mu – misali saboda ka taba yin haka ko saboda ba ka bi kaidar kawo kanka ba etc. – za su iya saka ka kulle a kowane lokaci yayin tsarin Dublin. Dalilan kulle ka suna cikin dokar kasa. Babu wai dalili fiye da wadanda suke cikin sharia da za su iya sa a kulle ka.

Kana da damar da za a baka a rubuce dalilin da yasa za a kulle ka, da kuma damar kin aminta da kullewar. Kana kuma da damar taimakon mai sharia ida kana so ka yi karar kulewar

Idan an kulle ka yayi tsarin Dublin, lokacin tsarin naka zai kasance kamar haka:

- Za mu bukaci wata kasar ta karbi hakkin a tsakanin **wata** na ajiye takardar neman damar kafarka.
- Dole ne kasar da muka aika wa bukatar ta mayar da martani tsakanin **sati 2** na karbar bukatar.
- Za a aiwatar da mayarda kai tsakanin **sati 6** na amincwa da bukatar kasar da ke da hakki tayi. Idan ka yi korafi akan shawarar mayar da kai, za a kirga sati 6 daga lokacin da hukumomin, ko kotu ko majlisar masu sharia tayi shawarar cewa ya dace a mayar da kai kasar da ke da hakkin yayin da ake duba daukaka kararka.

Idan muka kasa cinma kayadadden lokacin aikawa da wannan bukata ko aiwatar da mayarda kai, kulle ka domin mayarwa a tsarin Dublin za kare. A wannan yanayi, takaitaccen lokacin da aka nuna a sama za kasance.

## “Menene zai faru da bayanai na da na bayar? Ta yaya zan sani cewa ba za wulakanta min su ba?”

Hukumomin kasashent Dublin na iya canja bayanan da ka ke basu yayin tsarin Dublin domin cinma aikin da yarataya akansu a karkashin dokar Dublin da Eurodac. Gabadaya a cikin tsarin Dublin kana da damar kariya ga bayanai na kanka da na halin da iyalanka suke etc. Za a iya anfani da bayaninka ne akan abin da ya shafi doka kawai ne.

Za ka sama damar iso ga:

- Bayanan da suka shafe ka. Kana da damar da za ka bukaci cewa a gyara wannan bayanin, tare da batanan Eurodac idan ka yi kuskure, ko a share su idan ba a shirya su daidai ba;
- Zuwa ga bayanan dake bayani akan yarda za a tambaya cewa an gyara ko share bayananka, tare da bayanan Eurodac. Wannanya hada da bayana abokan ma’amala hukumar da ke kula da tsarin Dublin naka, dakuma hukumar kula da kariyar bayanan kasa da ke hakkin kula da bukatun kariya bayanan kai.

1.9.2016 hausa

European Commission

MAAHANMUUTTOVIRASTO
MIGRATIONSVERKET
FINNISH IMMIGRATION SERVICE